# SŨRATUT TĨN سُورَةُ التِّينِ

Tana karantar da cẽwa duka abin da ya shãfi addini bã ya halaka, sauran abubuwa suna halaka da shuɗẽwar zãmaninsu.

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

*1.* Inã rantsuwa da Attinu da Azzaitũn.[1]

وَٱلتِّينِ وَٱلزَّيۡتُونِ ١

*2.* Da Ɗũr Sĩnĩna.[2]

وَطُورِ سِينِينَ ٢

*3.* Da wannan gari[3] amintacce.

وَهَٰذَا ٱلۡبَلَدِ ٱلۡأَمِينِ ٣

*4.* Lalle ne Mun halitta mutum a cikin mafi kyawon tsayuwa

لَقَدۡ خَلَقۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ فِيٓ أَحۡسَنِ تَقۡوِيمٖ ٤

*5.* Sa'an nan Muka mayar da shi mafi ƙasƙantar masu rauni

ثُمَّ رَدَدۡنَٰهُ أَسۡفَلَ سَٰفِلِينَ ٥

*6.* Face waɗanda suka yi imani, kuma suka aikata ayyukan ƙwarai, saboda haka suna da sakamako wanda bã ya yankewa.

إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فَلَهُمۡ أَجۡرٌ غَيۡرُ مَمۡنُونٖ ٦

*7.* To, bãyan haka mẽ ya sanya ka ka ƙaryata sakamako (wanda za a yi a bãyan Tãshin Kiyãma)?

فَمَا يُكَذِّبُكَ بَعۡدُ بِٱلدِّينِ ٧

*8.* Ashe, Allah bã Shi ne Mafi mãsu hukunci kyãwon hukunci ba?[4]

أَلَيۡسَ ٱللَّهُ بِأَحۡكَمِ ٱلۡحَٰكِمِينَ ٨

---

(1) Ibn Abbas ya ce Attinu shi ne masallacin Nuhu a kan Judiyyi, Azzaitun Masallacin Baitil Muƙaddas.

(2) Dutsen da Allah Ya yi magana da Musa a kansa. Ma'anarsa dutse mai albarka sabõda itacen da ke kansa.

(3) Gari amintacce shi ne Makkah.

(4) Ana son wanda ya karanta sũrar har ƙarshe ya ce بلى Wato na'am, Allah Ya fi kowa kyãwon hukunci.